
# ILIMANTAR DA
# ALʼUMMA KAN KASAFIN KUƊIN JIHAR YOBE
# NA SHEKARA TA DUBU BIYU DA ASHIRIN
# (2020):



**MA'AIKATAR KASAFI DA TSARA TATTALIN ARZIQI TA JIHAR YOBE CE, TA TSARA, TA** KUMA BUGA A WATAN JANAIRU, SHEKARA TA 2020.

**HAKKIN MALLAKA**


Doka ta hana sake buga wannan littafi ko kuma ciran wani yanki domin sayarwa ba tare da samun izini a rubuce daga ma'aikatar kasafi ta jiha ba.

Mai amfani na iya buga littafin domin rabawa jama'a kyauta ta hanyar da ba zai nuna cewar ma'aikatar kasafi ta amince da hakan ba.

Ma'aikatar na iya ɗaukar kowane mataki na shari'a da ya dace da doka idan aka saɓawa ƙa'idarta

Ana iya samun cikakken bayani kan kasafin kuɗin a yanar gizo kamar haka: https://budget.pfm.yb.gov.ng

# KASAFIN SHEKARA TA DUBU BIYU DA ASHIRIN (2020), KASAFIN CI GABA DA AYYUKAN JIHA




*Mai Girma Gwamnan Jihar Yobe Hon Mai Malah Buni yana miƙa kasafin kuɗi na shekarar dubu biyu da ashirin (2020) ga majalisar dokoki na jihar Yobe a ranar Laraba 13 ga watan Nuwamba shekara ta dubu biyu da sha tara (2019)*

## MUƘADDAMA

Kasafin kuɗi na Jihar Yobe ya tsara hanyar yadda gwamnatin jiha ta yi niyar samar da kuɗaɗe da hanyar yadda za a yi amfani da su wajen gudanar da ayyuka na kyautata rayuwar 'yan ƙasa.

A zaman makoma ta tabbatar da tsare-tsaren gwamnati na ci gaba, yana da muhimmanci jama'a su fahimci irin rawa da kasafi ke takawa musanman wajen aiwatar da shi da kuma irin rawa da ya kamata su taka cikin aiwatar da kasafin. Idan har ya kasance jama'a ba su fahimci menene kasafin ba, zai rage koƙarinsu wajen shiga a dama da su da kuma gaza nuna kasawar Gwamnati wajen yin amfani da kuɗi da aka danƙa mata amanarsu.

Domin amincewa da matsayin jama'a da amincewa da Gwamnati, jihar Yobe ta ɗauki mataki na samar da kundin kasafi a saukake ga jama'a ta yadda za su fahimci kasafin shekara ta dubu biyu da shirin (2020) wanda aka yi masa laƙabin "KASAFIN CI GABA DA AYYUKA DA KUMA GIRBAR RIBAR".

Gwamnatin jihar Yobe ta duƙufa wajen samar da tsare-tsare kyawawa da aiwatar da su domin magance manyan buƙatun jama'a ta fannin aikin noma, da ilimi, da kula da lafiya, da samar da ruwan sha, da kayan more rauyuwa ga jama'a.

**Hon. Mohd Garba Gagiyo**
Kwamishinan Ma'aikatar Kasafi ta
Jihar Yobe

## ABUBUWAN DA KE CIKI.

Muƙaddama..........................................................................iv

Abubuwa da ke ciki...................................................................v

Gabatarwa............................................................................1

Matakan tsara kasafi.................................................................2

Taƙaitaccen bayani kan kasafin shekara ta 2016 2020........................3

Manyan abubuwa da ake tsinkaya da tanadi na tattalin 2020..............4

Inda aka sa gaba na kasafin 2020 ...............................................5

Daga ina za a samo kuɗin kasafin 2020 ..........................................6

A ina za a kashe kuɗin ..............................................................7

Rabo ga sassan ma'aikatu cikin kasafin 2020...................................8

Ma'aikatu da hukumomi da ke kan gaba wajen samun kaso ..............9

Manyan ayyuka da aka sa a gaba...................................................10

Kammalawa ..........................................................................13

Ma'anar kalmomi da aka yi amfani da su a kasafi............................14

## GABATARWA

Menene Kasafin kuxi na Gwamnati?

- Shi ne tsari ta yadda gwamnati ke samar da ƙuɗaɗen shiga ta hanya dabam-dabam domin gudanar da aiyukanta.
- Haka nan tsari ne na ƙudurorin gwamnati ga wasu shirye-shirye da kuma ayyuka wadanda ake nufin samar da ayyuka masu inganci da inganta tattalin arzikin rayuwar jama'a, da kuma rance da gwamnati take karɓowa ko biyan basussukan da ta ke yi.

Buqatar yin kasafi a jiha, na qunshe cikin doka ta tsarin mulkin Nijeriya, sashe na 121 karamin sashe cikin baka na (1) na tsarin mulki inda yace, Gwamna zai miƙa kasafin kuɗi na jiharsa gaban majalisar dokoki na jiha a kowane lokaci kafin farkon kowace shekarar kuɗi istimatin kuɗi da zai shigo wa gwamnati da wanda zai kashe a jihar na shekarar da za ta shigo".

Kasafi da ake yiwa 'yan kasa bayani ne mai sauki kan kasafin da gwamnati ke tsarawa ta samar da muhimman bayanai da jama'a za su fahimta.

# MATAKAN TSARA KASAFI

**Mataki na 1**
Sake dubawa da kuma samar da matsaƙaitun dabaru na ci gaban jiha (MTSS)

**Mataki na 2**
HarhaƊawa da shirya takardu da suka dangana dokar kasafi.

**Mataki na 3**
Gabatarwa gaban majalisar zartarwa ta jiha domin ta amince.

**Mataki na 4**
Ma'aikatar kasafi ta haɗu da masu ruwa da tsaki da kungiyoyi masu zaman kansu da kungiyoyin al'umma da ma'aikatu da hukumomi

**Mataki na 5**
Majalisar zartawa ta amince da takardar da aka miƙa mata

**Mataki na 6**
Sai a miƙa takardar ga majalisar dokoki domin neman amincewarta

**Mataki na 7**
Sai a rubuta takardar gyayyata ga ma'aikatu da hukumomin gwamnati domin su san abinda aka amince masu.

**Mataki na 8**
Kowace ma'aikata da hukuma ta gwamnati ta kawo jerin abinda za ta yi da kuɗin

**Mataki na 9**
Sai a shiga tattaunawa da hukumomi da ma'aikatu.


**Mataki na 10**
Harhaɗa kasafin ma'aikatu da hukumomin gwamnati

**Mataki na 11**
Majalisar zartawa ta sake duba kasafin da aka miƙa mata ta amince da shi

**Mataki na 12**
Gwamna sai ya miƙa kasafin gaban majalisa a zaman doka, majalisa ta duba ta tace ta amince da sunan dokar kashe kuɗi.

**Mataki na 13**
Daga karshe a kawo wa Gwamna ya sanya hannu ta zamo doka


# TAƘAITACCEN BAYANI KAN KASAFIN KUƊIN SHEKARA TA DUBU BIYU DA SHA SHIDA (2016) ZUWA DUBU BIYU DA ASHIRIN (2020).




| | 2016 | 2017 | 2018 | 2019 | 2020 |
|---|---|---|---|---|---|
| Amintaccen Kasashi | 88.93b | 82.57b | 92.18b | 91.65b | 108.31b |
| Kudin da Aka Kashe | 53.41b | 68.20b | 69.45b | 79.48b | 0.00b |




## MANYAN HANYOYI DA AKE TSIKAYAR SAMAR DA KUƊI DA TANADI NA TATTALI A SHEKARA TA 2020.




**INDA AKA SA GABA A KASAFIN 2020.**


- Jajircewa wajen farfaɗo da sashen ilmi.
- Inganta aikin noma ta hanyar rungumar tsarin noma na zamani domin sayarwa. Wannan gwamnati za ta matsa wajen tabbatar da samar da abinci, da samar da hanyoyi, da inganta arziki da taimakawa matasa su dogara da kansu.
- Samar da hanyoyin inganta kiwon lafiya cikin sauƙi ga jama'ar mu ta hanyar ɗaga martabar cibiyoyin kula da lafiya da tabbatar da cewa asbitocinmu da ɗakunan shan magani da cibiyoyin kiwon lafiya sun sami kulawa ta musanman da kuma magunguna da suka dace.
- Za a gina hanyoyi da samar da ruwan sha da inganta muhalli da hasken wutan lantarki a karkara da koƙari na sake tsugunar da mutane, gina matsuguni ga jama'a da taimaka masu su farfaɗo daga firgici na ta'addanci, da taimakawa zaman lafiya.
- Mayar da hankali wajen cin moriyar ma'adinai da muke da su, da wuraren shaƙatawa, da inganta ciniki da kasuwanci ta hanyar kyautatawa domin a samo 'yan kasuwa masu zaman kansu su zuba jari da kafa masana'antu.

## HANYOYIN SAMO KUƊAƊEN.





## A INA ZA A KASHE KUƊIN







## KASO GA SASSAN MA'AIKATU A KASAFIN 2020




## MA'AIKATU DA KE GABA-GABA A KASO




## MA'AIKATU DAKE GABA-GABA A KASO



# MANYAN AYYUKA DA AKA KIRƘIRO A KASAFIN DUBU BIYU DA ASHIRIN (2020)



## GWAMNATI DA TAFIYAR DA MULKI

### OFFISHIN SAKATAREN GWAMNATI



| | |
|---|---|
| SAYAN MOTOCI | ₦1,300,000,000 |
| GINA GIDAJE | ₦ 400,000,000 |
| GYARAN GIDAJE | ₦ 300,000,000 |

### YAƊA LABARAI



| | |
|---|---|
| - GINA OFFISHIN RADIO A SHIYOYI UKU NA JIHA | ₦240,000,000 |
| - SAYAN KWAMFUTA A YTV DA YBC | ₦200,000,000 |

### AIKIN GONA



| | |
|---|---|
| SAYO KAYAN AIKIN NOMA (MotocinTantan) | ₦500,000,000 |
| SAYO KAYAN SAMAR DA RUWA (INJINAN BAN- RUWA DOMIN MANOMA) | ₦200,000,000 |
| GINA MATARAR RUWA, DAM-DAM DOMIN AIKIN NOMAN RANI | ₦340,000,000 |
| SAYO TAKIN ZAMANI | ₦400,000,000 |

## CINIKI DA MASANA'ANTU




| | |
|---|---|
| - GINA KASUWAR ZAMANI A DAMATURU, BUNIYADI DA WASU GUDA BIYU A POTISKUM DA GASHUA | ₦4,000,000,000 |
| - SAYO KAYAN MASANA'ANTU | ₦ 100,000,000 |

## SUFURI DA MAKAMASHI



| | |
|---|---|
| KARASA GINA FILIN SAUKAR JIRGIN SAMA NA DAKON KAYA A DAMATURU | ₦6,000,000,000.00 |
| SAMAR DA HASKEN WUTAN LANTARKI A KARKARA | ₦ 390,000,000.00 |
| SAYO INJINAN BADA HASKEN LANTARKI | ₦ 150,000,000.00 |

## AYYUKA



| | |
|---|---|
| GYARAN HANYOYI | ₦1,100,000,000.00 |
| GINA SABIN HANYOYI | ₦5,500,000,000.00 |
| GINA KWABATOCI DA MAGUDANAN RUWA A JIHA | ₦ 140,000,000.00 |
| SAYAN MANYAN KAYAN AIKI KAMAR SU BULDOZA DA DAI MAKAMANTANSU | ₦ 200,000,000.00 |

## MA'AIKATAR RUWA



| | |
|---|---|
| SAMAR DA RIJIYOYIN BURTSATSE DA SAURAN KAYAN NA RUWA | ₦960,000,000.00 |
| KAYAN SAMAR DA RUWA | ₦ 80,000,000.00 |
| SAYO KAYAN SAMAR DA RUWA | ₦ 40,000,000.00 |

## MA'AIKATAR ILIMI



| | |
|---|---|
| GINA AZUZUWA | ₦1,200,000,000 |
| SAKE GYARA GINE-GINE NA MAKARANTA A FAƊIN JIHA | ₦1,300,000,000 |
| BIYAN KUƊIN JARRABAWA NA DALIBAI DA YI MASU RAJISTA | ₦ 703,000,000 |
| BIYAN KUƊAƊEN TALLAFI GA DALIBAI CIKI DA WAJEN KASA | ₦ 400,000,000 |
| SAYAN KAYAN ABINCI DOMIN CIYAR DA ƊALIBAI | ₦1,000,348,000 |

## MA'AIKATAR KIWON LAFIYA



| | |
|---|---|
| GINAWA, DA SAMAR DA KAYAN KULA DA LAFIYA A ASIBITOCIN BARA, MACHINA DA KARASUWA | ₦800,000,000 |
| GYARA DA KWASKWARIMA GA GINE-GINAN ASIBITOCI | ₦500,000,000 |
| SAYO KAYAN KULA DA KIWON LAFIYA DA DAKUNAN BINCIKE | ₦600,000,000 |
| SAYO MAGUNGUNA DA KAYAN DAKUNAN BINCIKE DON BAYARWA KYAUTA | ₦260,000,000 |

## KAMMALAWA

Manufar kasafi shekara ta dubu biyu da ashiri (2020) ita ce tabbatar da irin ci gaba da aka samu da farfaɗowa da ƙarasa ayyuka da da gwamnati ta fi ba da fifiko a kansu a shekara ta dubu biyu da goma sha tara (2019) kamar su ilimi, da kiwon lafiya, da aikin gona da kayan kyautata Jin daɗin rayuwa, da ƙirƙiro wuren aiki, da masana'antu da samar da sabbin dabaru.

Ta wannan hanyar za a ci gaba da sanar da jama'a yadda ake tafiyar da dukkan ɓangarorin kasafin da yadda ake amfani da kuɗin, domin su kasance suna sane, kuma su bibiyi yadda ake tafiyar da kasafin domin su sami damar ba da shawarwari masu ma'ana.

Koƙari da ma'aikatar kasafi da tsara tattali da majalisar dokoki na jihar yobe ke yi wajen jawo jama'a ana tattaunawa da su wajen tsara kasafin abin yabawa ne , kuma wannan sannu a hankali na sanya jama'a fahimtar yadda ake tsara kasafin kuɗi da kuma ma'anarsa.

Daga ƙarshe, ana shawartar jama'a su ci gaba da shiga cikin harkar tsara kasafi da nufin shigar da buƙatunsu ciki, yayinda ake shirya kasafi a kowace shekara.

## FASSARAR KALMOMI DA AKE AMFANI DA SU CIKIN KASAFI

- **Accountability** : Ma'anarta ita ce inda Gwamnati za ta rinƙa bayani kan yadda ta ke amfani da dukiyar jama'a kuma yi masu bayani kan sakamako da aka samu.
- **Budget Deficit**: Giɓi da aka samu bayan Gwamnati ta yi kasafin kuɗi da ake sa ran samu.
- **Budget Surplus**: Ragowar da aka samu daga kuɗaɗen Gwamnati da ta lissafa za ta kashe ko kuma a ce rara da aka samu.
- **Budget Policy Statements (BPS):** Tsari ne na tabbatar da niyar Gwamnati kan bin dokar kasafi da ta yi, wanda ya haɗa abin da ta zana za ta yi, ƙa'idojin tsare-tsare na EFU da FSP da ke cikin kasafin shekara, da tsara abinda za a kashe na kimanin shekaru uku a ɓangarorin ma'aikatu na manyan ayyuka ko kuma manyan ayyuka da ayyukan yau da kullum dabam-dabam waɗanda aka shirya aka amince kafin rubuta takardar gayyata ga ma'aikatu a zo a shirya kasafin shekarar.
- **Capital Expenditure :** Kuɗi da Gwamnati ke samarwa kan manyan ayyuka kamar gina kwalbatoci da gadoji da hanyoyi da makarantu da asibitoci da magudanun ruwa da sayo motoci da samar da ruwan sha da hasken wutan lantarki da dai sauran makamantansu.
- **Consolidated Revenue Fund (CRF):** Kuɗaɗe da Gwamnati ke biya ga hukumomi da ta kafa kamar su hukumar zaɓe ta jiha, da ofishin babban mai binciken kuɗin gwamnati da alkalai da 'yan majalisar dokoki da majalisar zartarwa ta jiha da dai sauransu.
- **Economic And Fisical Update**: Tsokaci da ake yi kan tattalin arziƙi, wanda da shi ne ake duba tsarin kasafin kuɗi. Wannan ya shafi jami'an gwamnati ne a jiha kuma ya kan zamo hanyar ƙalelece kasafi a ga inda nasara ta samu da inda aka gaza da nufin ɗaukar mataki.
- **Fiscal Strategy Papers (FSP):** Wanan hanya ce da ta daganci yadda gwamnati ke duba dabarun samar da kasifin ta hanyar duba kuɗaɗen shiga, yadda ake kashewa da kuma abin da ya rage harma da hanyar samun bashi. Wadanan su ake sakawa cikin kasafi a kowace shekara.

- **Grants**: Taimako da ake samu na kuɗi daga cikin gida ko waje wa gwamnati domin aiwatar da wasu aiyuka.
- **Gross Domestic Product (GDP)**: Adadin kuɗi da ake samu kan kayak o aiyuka da 'yan jiha ko ƙasa ke samu a shekara.
- **Inflation**: Hauw-hawan farashin kaya da ake samu daga lokaci zuwa lokaci.
- **Macroeconomic Framework:** Tsari ne da ke samarda cikakken bayani kan tattali inda ake tsokaci kan tattalin ƙasa da ya shafi siyasa, da al'amuran yau-da kulum a duniya ko ƙasa da kuma matakin jihohi da ya ke zama jagora ga tattalin arziki na jiha da yadda ake amfani da kuɗin jiha.
- **Medium Term Expenditure Framework (MTEF):** Wanan tsari ne da gwamnati kan yi wajen tsara kasafi ta hanyar sanya kuɗi kan kowane aiki da za ta aiwatar kan aikin da ta bada fifiko da tabatar da bin tsari da dokar yin anfani da dukiyar gwamnati.
- **Medium Term Sector Strategies (MTSS):** Tsari ne da ake yi na kamar shekara uku da gamnati za ta aiwatar, cikin tsarin gamnati za ta bayana kuɗi da za a kashe kan kowane aiki, da wa zai yi akin, da inda za a samo kuɗin, da tsinkayar matsala da za a fuskanta.
- **Overhead Cost:** Kuɗi da gwamnati ke kashewa na yau-da kulum wajen aiki da kuma jin daɗin ma'aikata.
- **Personnel Cost:** Kuɗaɗen albashi da sauran alawus-alawus da gwamnati ke kashewa haɗa da kuɗaɗen sallama ga ma'aikata.
- **Transparency:** Hanya ce da gwamnati ke bada sahihin labarin aiyukan da take gudanarwa cikin lokaci domin jama'a su san abin da take yi.

- **Value Added Tax (VAT):** Harajin kaya da aka saya
- **Fiscal Strategy Papers (FSP):** Wanan hanya ce da ta daganci yadda gwamnati ke duba dabarun samar da kasifin ta hanyar duba kuɗaɗen shiga, yadda ake kashewa da kuma abin da ya rage harma da hanyar samun bashi. Wadanan su ake sakawa cikin kasafi a kowace shekara.
- **Grants**: Taimako da ake samu na kuɗi daga cikin gida ko waje wa gwamnati domin aiwatar da wasu aiyuka.
- **Gross Domestic Product (GDP)**: Adadin kuɗi da ake samu kan kayak o aiyuka da 'yan jiha ko ƙasa ke samu a shekara.
- **Inflation**: Hauw-hawan farashin kaya da ake samu daga lokaci zuwa lokaci.
- **Macroeconomic Framework:** Tsari ne da ke samarda cikakken bayani kan tattali inda ake tsokaci kan tattalin ƙasa da ya shafi siyasa, da al'amuran yau-da kulum a duniya ko ƙasa da kuma matakin jihohi da ya ke zama jagora ga tattalin arziki na jiha da yadda ake amfani da kuɗin jiha.
- **Medium Term Expenditure Framework (MTEF):** Wanan tsari ne da gwamnati kan yi wajen tsara kasafi ta hanyar sanya kuɗi kan kowane aiki da za ta aiwatar kan aikin da ta bada fifiko da tabatar da bin tsari da dokar yin anfani da dukiyar gwamnati.
- **Medium Term Sector Strategies (MTSS):** Tsari ne da ake yi na kamar shekara uku da gamnati za ta aiwatar, cikin tsarin gamnati za ta bayana kuɗi da za a kashe kan kowane aiki, da wa zai yi akin, da inda za a samo kuɗin, da tsinkayar matsala da za a fuskanta.

- **Overhead cost:** Kuɗi da gwamnati ke kashewa na yau-da kulum wajen aiki da kuma jin daɗin ma'aikata.

- **Personnel cost:** Kuɗaɗen albashi da sauran alawus-alawus da gwamnati ke kashewa haɗa da kuɗaɗen sallama ga ma'aikata.

- **Transparency:** Hanya ce da gwamnati ke bada sahihin labarin aiyukan da take gudanarwa cikin lokaci domin jama'a su san abin da take yi.

- **Value Added Tax (VAT):** Harajin kaya da aka saya